## EPISODE 15

**Characters**

*Tina*

*Hannah*

*Danjuma*

*Dr. Daoud*

*Laraba*

---

**Scene 1**

**Northern Kaduna, Danjuma's house.**

| | | |
|---|---|---|
| 1. | **MUSIC:** | **THEME MUSIC** |
| 2. | **SFX:** | **SOUNDS OF WASHING PLATES.** |
| 3. | **TINA:** | (**HUMMING A ROMANTIC LYRIC**) *You don make me fall in love, make me fall in love…* |
| 4. | **HANNAH:** | (**INTERRUPTS**) ke kuma me kike yi a kicin di na Tina? |
| 5. | **TINA:** | **(EXCITED**) Ah Hannah! Babbar yayata, na girka abincin yamma ne. menene ya faru? |
| 6. | **HANNAH:** | Haba! Kin kyauta. Daba ki ba kanki wuya baa i. kin san nafi son in girka abincin mai gidana ai |
| 7. | **TINA:** | E na san hakan. Amma ranar da ya dawo da ga tafiya a ci raguwar dafa dukan shinkafar da na girka kuma ya ji dadin sa kwarai. Sai yasa nace in sake girka irin dafadukar |
| 8. | **HANNAH:** | **(IRRITATED)** Haka akayi tina? Gaskiya da baki takura kanki ba fa. |
| 9. | **TINA:** | Ai ba takura ce ba ai, yayata Hannah. |
| 10. | **HANNAH:** | Nagode kwarai Tina, amma nan gaba kada ki saki girka abincin mai gida na kuma, nafi son in girka abincin sa. |
| 11. | **TINA:** | **(SURPRISED)** Amma don Allah, saboda menene hakan? Kuma inna taimakawa ne saboda yanayin da keki ciki na juna biyu, ina ganin kamar kina bukatar a taimaka meki |

| | | |
|---|---|---|
| 12. | **HANNAH:** | **(SERIOUS)** Tina nagode kwarai don taimaka min da kike yi anan gidan. Amma dai don Allah ki kyale girkin abincin majina mani, ne dai nafi son in yi masa abinci da kaina |
| 13. | **TINA:** | **(SARCASTICALLY)** Kiyi hakuri, ni dai taimako nake yi . |
| 14. | **MUSIC:** | **BRIDGE MUSIC** |

**Scene 2**

**Northern Kaduna. Hajiya Inna's House: Exterior. Evening.**

| | | |
|---|---|---|
| 15. | **SFX:** | **SOUNDS OF CRICKETS CROAKING. OCCASIONAL SOUND OF ROAD TRAFFIC UNDERLAYS SCENE** |
| 16. | **LARABA:** | **(LAUGHING)** Kai Dacta Daoud, kana da abin ban dariya |
| 17. | **DR. DAOUD:** | **(LAUGHING)** Da gaske na ke Laraba, sai kin gan yadda Matron din ta kale ne dana subda farantin magungunan ta. Kuma ina dalibin likita lokacin, naji tsoro kwarai fa. . |
| 18. | **LARABA:** | **(STILL LAUGHING)** Ah Daoud, kamar kana da tarihi ban sha'awa alokacin ka na makarantar koyan aiki likitanci. |
| 19. | **DR. DAOUD:** | Gaskiya Laraba, na ji dadin makarantar kwarai, na tabbata kema kina da ababen ban sha'awa dama ai ? |
| 20. | **LARABA:** | **(UNCOMFORTABLE)** Ummm ba sosai daoud. Na mance da wadancen lokutan ma. |
| 21. | **DR. DAOUD:** | Haba Labara. Me yasa duk lokacin da na so in san wani abu game da ke, sai ki kauce? |
| 22. | **LARABA:** | Ba kaucewa bane Daoud, bana cika son magana game da rayuwa ta ne, ba wani abun ban sha'awa aciki ai . |
| 23. | **DR. DAOUD:** | Toh, amma me yasa kice kadai macen da bazan iya kyale w aba. Ko na gwada bazan iya ba laraba |
| 24. | **LARABA:** | **(SMILING)** Daoud, kana ban mamaki wasu lokutan, kana yi kamar dan siyasa |
| 25. | **DR. DAOUD:** | (**SERIOUS**) Wallahi da gaske nake, ba siyasa bace, ko zakin baki don ki aminci da ni laraba |
| 26. | **LARABA:** | Toh Daoud na ji . |
| 27. | **DR. DAOUD:** | Kina jina Laraba, wannan soyarya ta mu bana wasa bane fa, ina son tafi haka fa. Ina son abin dindin din ne fa. |

| | | |
|---|---|---|
| 28. | **LARABA:** | **(NERVOUSLY)** Daoud nima hakan nake so, amma bani da tabas cewa a shiryi nake. |
| 29. | **DR. DAOUD:** | shirin mai kuma? Idan kina mutukar sona kamar yadda nake son ki, toh ai sai ki aminci ayi |
| 30. | **LARABA:** | **(PLEADING)** Don Allah Daoud ina bukatan dan lokaci kadan |
| 31. | **DR. DAOUD:** | Ba matsala Laraba, ki dai san cewa duk lokacin da kika yanke sharawa ina nan. Abin farin ciki shine muna kaunar juna |
| 32. | **LARABA:** | Na gode |
| 33. | **DR. DAOUD:** | Haba! Ai komai zan iya yi maki. **(HAPPILY)** yauwa, ki fada min, yaya nauwa zaki so ki Haifa? |
| 34. | **LARABA:** | **(SURPRISED)** Yaya?! Tun yanzu?! Bamu je ko ina a wannan soyayar tamu bafa |
| 35. | **DR. DAOUD:** | Laraba *kenan.* Ai don ki san cewa da gaski nake, ina son mu dinga yanke shawarwari tare |
| 36. | **LARABA:** | Daoud, kayi hakuri bawai ina shakkar ka bane, ban yi zaton zaka yi zancen yanzu bane |
| 37. | **DR. DAOUD:** | Ba matsalla, ban ji haushi ba, amma dai ki fada min yaya nawa kike so? |
| 38. | **LARABA:** | **(SMILING)** Tor, ina laifin uku (3). |
| 39. | **DR. DAOUD:** | Yayi, basu yi yaw aba basu kuma kasa ba, za ki so ki yi tazarar haihuwa ko zaki so ki yi lokaci daya ki huta **(LAUGHING)** |
| 40. | **LARABA:** | **(LAUGHING LIGHTLY)** Ahh ahh, sam sam, hikimar Haifan gaba day aa huta bai dace da lafiyan jiki ba ai, ne dai zany i tazarar haihuwa! Bana son in takura ma jiki na |
| 41. | **DR. DAOUD:** | **(LAUGHING)** ai baa bin tada jijiyar wuya bane, tabbaya ce kawai. |
| 42. | **LARABA:** | **(LAUGHING TOO)** Daoud na san tsokana ta kake yi ai, saboda ka dai san ai ni zany i amfani da hanyar tazarar haihuwa. Idan ban yi ba ina amfanin nuna wa wasu mata muhimmuncin tazarar haihuwa, ai ya dace su gane a wuri na . |
| 43. | **DR. DAOUD:** | Hmmm, gaskiyar ki, madallah tunanin mu tazo iri daya game da yaya mu da cin gaban su. Saboda inna burin kada su rasa komai a rayuwarsu, kama daga muhalli, abinci, ilimi, kai komai ma |

| | | |
|---|---|---|
| 44. | **LARABA:** | Da dukan alamu insha Allah ai zasu yi saar uba |
| 45. | **DR. DAOUD:** | na'am Insha Allah, ama kin mance da wani babbar abu |
| 46. | **LARABA:** | Menene? |
| 47. | **DR. DAOUD:** | baki ce zan kasance masoyi kuma maigida kwarai ba, saboda inna son mu iya tattauna ba tare da shakka ba, mu zama tamkar abokai |
| 48. | **LARABA:** | gaskiyar ka, hakan na taimaka ma ma'aurata su kusance juna kwarai |
| 49. | **DR. DAOUD:** | **(SMILING)** kamar yadda muke gina tamu yanzu ko? |
| 50. | **LARABA:** | **(LAUGHING SHYLY)** Ai na fada maka cewa kai dan siyasa ne, ka iya Magana Daoud |
| 51. | **DR. DAOUD:** | Idan har siyasar tana burge ki, toh ai yanzu na soma kenan |
| 52. | **LARABA:** | Nima haka Daoud. |
| 53. | **DR.** DAOUD: | Kuma ina jin dadi muna tattaunawa haka, idan harm un chigaba da hakan baza mu sami matsala nan gaba ba. |
| 54. | **MUSIC:** | **BRIDGE MUSIC** |

**Scene 3**

**Northern Kaduna. Danjuma's House. Late Afternoon.**

| | | |
|---|---|---|
| 55. | **SFX:** | **SOUND OF DOOR OPENING AND CLOSING.** |
| 56. | **TINA:** | Barka da dawowa, yaya Danjuma |
| 57. | **DANJUMA:** | **(COMING ON MIC)** Yauwa Tina, Inna Hanna take? |
| *58.* | **TINA:** | Ta kai ziyara zuwa wurin kawarta Laraba, amma tace baza ta dadai ba. |
| 59. | **DANJUMA:** | Yayi, ba matsala |
| 60. | **TINA:** | Yaya danjuma, Bara in kawo maka abincin ka kafin ka shanja kayan ka, |
| 61. | **SFX:** | **SOUND OF SHUFFLED FEETS AS TINA MAKES TO LEAVE** |

62. **DANJUMA:** A'a, kada ki damu Tina, zan jira matata ta dawo kafin in ci abinci.

63. **TINA:** **(CUTS IN)** Amma Yaya, ta aminci in baka abinci ka kafin ta dawo fa.

64. **DANJUMA:** Hmmm, duk da haka zan jira ta, saboda ai tare muke cin abinci, kada ki damu .

65. **TINA:** **(DISAPPOINTED)** Toh, tunda k adage ba damuwa. Daman ina son in taimaka ma yar'uwata Hanna ce, kuma ganin ka dawo a gajiye bai kamata ka sake zama da yinwa ba a i

66. **DANJUMA:** Hmmm, nag ode Tina, mun tsaba cin abinci tare ne shi ya sanya .

67. **TINA:** Na gane yaya, kuma hakan yana da kyau

68. **DANJUMA**: amma ba wai bana jin dadinn tallafin da kike yi mana bane fa, abinda Hannah ki bukata kwarai ma a yanzu da take da babbar ciki

69. **TINA:** Ai yar'uwa ta ce, kuma kai ma yaya Danjuma, ka yi min kirki sosai ai, ka bani aiki a ofisin ka, kuma kana kyauta min….

70. **DANJUMA:** Toh, ai ba wani abu bane, Tina ce ta nuna min ya dace ayi hakan nima sai na aminci.

71. **TINA:** Duk da hakan, nagode yaya Danjuma

72. **DANJUMA:** **(SMILING)** Tina ki gode wa Allah

73. **TINA:** **(CLEARS THROAT)** Toh, har yanzu sai Hannah ta dawo zaka ci abincin? Irin dafa dukan shinkafar da kace tayi dadin nan ne fan a girka

74. **DANJUMA:** E, kamar yadda na fada miki, zan jira Hannah ta dawo, bara in shiga daki in…..

75. **TINA:** **(INTERRUPTS)** Duk da cewa nina girka abincin yaya Danjuma?

76. **DANJUMA:** **(CURIOUS)** Toh Tina, menene a bincin idan ke kika girka?

77. **TINA:** Ba wani abu fa, dun dai ganin cewa yar'uwa bata nan ta kawo maka abincin ne kawai, **(SEDUCTIVELY)** Toh, amma kasan duk abinda da kake bukata ina nan

78. **DANJUMA:** **(AMUSED)** Kina da abin ban dariya Tina

| | | |
|---|---|---|
| 79. | **SFX:** | **<u>SOUND OF FEET SHUFFLING AS DANJUMA LEAVES</u>** |
| 80. | **DANJUMA:** | **(GOING OFF MIC)** Na gode, yanzu ya kamata in shanja kaya na in kuma huta, idan Hannah ta dawo ki fada mata inna ciki |
| 81. | **TINA:** | Na'am Yaya Danjuma, zan fada mata, ina jin dadin taimaka wa yar'uwata da kai ma |
| 82. | **MUSIC:** | **<u>BRIDGE MUSIC</u>** |

**Scene 4**

**Northern Kaduna. Hajiya Inna's House. Late Afternoon.**

| | | |
|---|---|---|
| 83. | **SFX:** | **<u>COMMOTION OFF MIC, DOOR SHUTS, SOUND OF ROOM AMBIENCE</u>** |
| 84. | **LARABA:** | **(ALMOST WHISPERING)** Kina ji na Hannah, haka na ke ta fama da Asabe, tana son rigima ba tare da dalili ba. |
| 85. | **HANNAH:** | *Toh, Allah kyauta* Amma shiya sa bana ganin ki sosai cikin yan kwanakin nan? |
| 86. | **LARABA:** | Amin yar'uwata, sam aikin asibitin ne ke dauke min lokaci, aikin na bukatan lokaci sosai kuma kin san inna harkan fadakarwa ta kungiyar lafiya ta al'umar |
| 87. | **HANNAH:** | Allah ya saka miki Laraba |
| 88. | **LARABA:** | **(AGREES)** Amin o, Hannah. Mu kyale zance nah aka, yaya kike fama da juna biyu |
| 89. | **HANNAH:** | **(SMILING)** A'a bani da matsala tare da cikin. Hankali na yafi tashi game da yar'uwataTina. |
| 90. | **LARABA:** | Tina? Menene matsala? Bata lafiya ne ko menene? |
| 91. | **HANNAH:** | A'a lafiyar ta **(WORRIED)** Ta shanja ne, ba kamar ida ta zo ba, tana wasu iriirn halayen da ban gane ba cikin yan kwanakin na. |
| 92. | **LARABA:** | Toh ai tunda tana matsayin yar karamar kan wanki ce, sai ke fada mata game da abinda take yi da baki jin dadi shi. |
| 93. | **HANNAH:** | Gaskiyar ki Laraba, nidai kin san ban cika son yawan maganganu ba, amma ina ganin hakan zan yi, nagode |

| | | |
|---|---|---|
| 94. | **LARABA:** | Haba! Hannah menene fa'idar abokantaka idan bazan baki shawara ba, |
| 95. | **HANNAH:** | Laraba, Baki yi zancen Dacta Daoud ba, ina fatan komai dai lafiya? |
| 96. | **LARABA:** | Komai lafiya, mutunin baisan a'a ko dan ban lokaci ba fa,. |
| 97. | **HANNAH:** | **(CONFUSED)** *Kamar yaya?* |
| 98. | **LARABA:** | Toh, yana ta matsawa inyi mai kwatacin wurin kawu na zasu je tambaya |
| 99. | **HANNAH:** | **(EXCITED)** Da gaske kike? Ai abin murna ne **(PAUSES)** Amma LAraba ai yakamata kiyi farin ciki ba wai kin a fada kamar kina fadar mutuwa ba. |
| 100. | **LARABA:** | **(WORRIED)** Hakane, tsoro nake ji kada Dacta Daoud yazo yam utu kamar su Jallo da saurar su **(CLOSE TO TEARS)** Hannah bazan iya jurewa ba kuma. |
| 101. | **HANNAH:** | **(CONCERNED)** Sam, baza ki sake shiga cikin irin wadanchan halayen ba kuma, komai zai tafi daidai yanzu |
| 102. | **SFX:** | **<u>SOUND OF LARABA'S SOFT SOBS AND BLOWING THE NOSE</u>.** |
| 103. | **HANNAH:** | **(COMFORTINGLY)** Kuma na san ki kwarai Laraba, baza kid age wa namiji ba in har ba sonsa kike yi ba . |
| 104. | **LARABA:** | E Hannah, ina mutukar son Dacta Dauod, sai yasa bana son wani abu ya faru da shi, ban san mai zai auko mas aba idan har y adage zai aure ni . |
| 105. | **HANNAH:** | Ina ganin, abinda yakamata ki yi shine ki fada masa abinda ya faru chan baya, wato har abinda ya sami Jallo, na tabatta hakan zai rage fargaban da kike fama da shi yanzu. |
| 106. | **LARABA:** | **(UNCERTAIN)** Hannah, kin tabbata hakan zai yi, bana son wani abu a sa in rasa Daoud. |
| 107. | **HANNAH:** | **(CONFIDENTLY)** Laraba kawata komai zai tafi daidai, amma na farko kuyi Magana da Daoud. |
| 108. | **MUSIC:** | **<u>THEME MUSIC</u>** |